# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Tuntuɓar juna tsakanin addinai: Haɗin kan mutanen Sodangi
## Kashi na shida: Konewar hannaye


| | |
|---|---|
| Wanda ya rubuta: | Romie Singh |
| Wanda ya tace: | Katrin Ogunsade, Naïma Guira |
| Wanda ya fassara: | Ɗanlami Bala Gwammaja |


**'Yan Wasa:**

| | |
|---|---|
| Malam Isma'ila: | ɗan shekara 43, baban Layla |
| Nas Rakiya: | 'yar shekara 28 |
| Hassan: | ɗan shekara 12, ɗan'uwan Layla |
| Layla: | 'yar shekara 16 |
| Dauda: | ɗan shekara 17 |
| Maigida Ranau: | ɗan shekara 51, baban Dauda |
| Maryam: | 'yar shekara 16 |
| Tafida: | ɗan shekara 17 |

**MAI GABATARWA:**
Masu sauraronmu, barkanmu da sake saduwa da ku a cikin wani sabon shirinmu na "Ji Ka Karu" mai taken "Haɗin kan mutanen Sodangi", wanda aka shirya a kan yadda addini da siyasa suka zama tarnaƙi a tsakanin wasu al'umma guda biyu, da kuma wasu gidaje biyu, da kuma tsakanin wasu matasa biyu, wato Dauda da Layla, waɗanda aka tilasta wa ɓoye soyayyar da suke wa juna. A wannan kashi na yau mai suna "Konewar hannaye" Hassan, ƙanen Layla, ya ƙi amincewa da maganin da likitoci suke ƙoƙarin yi masa. Shi kuwa Dauda yana ta ƙoƙarin kashe wuta dangane da aika-aikar da ya rigaya ya faru.

**MAI BA DA LABARI:**
Abin al'ajabin da ya faru a wannan dare, shi ne ya mamaye labarin da Jaridar Muryar Sodangi ta ɗauko. Kanun labarin da ke shafinta na farko cewa yake: "An cinna wa wata cocin wuta". A matsayin baban Tafida na babban editan wannan jarida, dole ya tabbatar da cewa wannan labari ya shiga cikin jaridar tasa. Shi kuma Hassan yana can yana kwance a asibiti saboda ƙonewar da ya yi. To da yake shekarunsa sha biyu ne rak, ya zama wajibi a kan jaridar kar ta bayyana wa jama'a, duk da cewa kowa ya san abin da ya faru. Su kuma 'yan sanda suna can suna jiran ya sami sauƙi su cafke shi. A can gidan su Hassan kuwa, babansa ya shiga wani hali na ruɗani, saboda ya kasa fahimtar abin da ɗan nasa ya aikata. Ina ma dai mahaifiyar Hassan tana nan da ranta, don kuwa yanzu ne yake matuƙar buƙatarta. A halin yanzu dai yayarsa Layla ita ta maye gurbin mahaifiyarsa, shi ya sa ma ta ɗan dakata da zuwa makaranta.

**Fitowa ta 1: A asibiti**
Nas Rakiya, Malam Isma'ila, Hassan

**NAS RAKIYA:** Sannunka dai Malam Isma'ila, sunana Rakiya. Ni ce nas ɗin da ke kula da ɗanka, kuma na lura ba ya cin abinci. Shi ya sa nake masa ƙarin ruwa.

**MAL. ISMA'ILA:** Yanzu kina ganin idan mun yi masa magana zai ji mu?

**NAS RAKIYA:** Ba na jin hakan. Ni abin da na lura shi ne, ba ya buƙatar mu taimaka masa.

**LAYLA:** Don Allah Hassan, ka yi magana mana. Ka ga fa yadda hannayenka suka ƙone. Kuma ga shi muna son mu ba ka abinci. Don Allah ka buɗe idonka.

**HASSAN:** Allahu Akbar. Ni ba wani kafiri da zai taimake ni.

**NAS RAKIYA:** Na gane abin da yake nufi. Yana nufin wai ni Bayahudiya ce. Ku bar shi ya ɗan huta. Ruwan da aka sa masa zai sa jikinsa ya daina yaushi.

**MAL. ISMA'ILA:** Ni kuwa don Allah Nas, a ina kike ganin ya ɗebo waɗannan munanan aƙidun nasa? Na tabbatar ba sa cikin Alƙur'ani Mai Girma. Kai Hassan! Buɗe kunnuwanka ka ji kuma da kyau!

**NAS RAKIYA:** Shhhh! Haba Malam Isma'ila, kada ka tashi hankalinka kuma ka tashi hankalin wannan mara lafiya. Ya kamata a bar shi ya ɗan huta.

**MAL. ISMA'ILA:** Layla, ya kamata ki zauna a wajensa! Ni ina da wani uzuri. Kin san yanzu yana buƙatar wadda za ta dinga kulawa da shi kamar mahaifiyarsa. Kuma don Allah, Layla, ki kula da shi yadda ya kamata har lokacin da zai dawo cikin hayyacinsa.

**MAI BA DA LABARI:**

Washegari da Tafida ya haɗa da Dauda a makaranta, irin damuwar da ta bayyana a fuskar Dauda ya tabbatar wa Tafida da cewa yanzu kome ya zo ƙarshe. Yanzu kawunsa ya ɗauki laifin kome ya ɗora a kan zuriyar Umaru, shi ma ya sa ya haramta wa Dauda haɗuwa da Layla bayan an tashi daga makaranta. Shi abin da Dauda yake nuna wa kawun nasa shi ne, cewa wasu matasa ne da ke makarantar Islamiyyar da Hassan yake zuwa, suka yi amfani da shi wajen cim ma wannan mugun manufa tasa. Wato dai sun sami yaro ƙarami ya zama sojan bante! Amma kawun nasa ya ƙi yarda da duk wannan uzuri. Don haka ma Dauda ke neman taimakon su Tafida da Ɗanjuma. Layla kuma ta nufi wajen Dauda don ya kwantar mata da hankali.

**Fitowa ta 2: A Kwalejin Zumunta**

Dauda, Layla (suna waya)

**DAUDA:** A'a, Layla! Kina jina Layla? Me yake faruwa ne. Kina lafiya kuwa?

**LAYLA:** Dauda, kana ji? Ni wallahi na ma rasa abin da zan ce. Na yi takaicin abin da ya faru. Don Allah ka yafe wa Hassan. Ka san shi…shi…

**DAUDA:** To ke kuma fa, Layla? Ba inda za mu haɗu ne? Ina so mu yi wata 'yar magana da ke.

**LAYLA:** A nan dai ni kaɗai ce. Amma ka san ba za a bar ni na kaɗaice da kai ba.

**DAUDA:** Layla, don Allah so nake mu yi magana da ke, ko a ina ne, minti biyar ma ya isa. Mu haɗu a ƙarƙashin gadar Sodangi mana.

**LAYLA:** Ai ba zai yiwu ba.

**DAUDA:** Kin ga, ba fa wanda zai gan mu: mutane ba sa wucewa ta wurin. Don Allah minti biyar ma kaɗai ya isa!

**LAYLA:** To na ji, amma don Allah Dauda, kar ya wuce minti biyar ɗin.

**MAI BA DA LABARI:**
Dauda ya roƙi abokansa da suka haɗa da Tafida da Ɗanjuma, da su yi masa aikinsa, don kuwa ba zai sami damar zuwa wajen atisayen ƙwallon ƙafar da yake zuwa ba. Shi dai Dauda yana ganin cewa ya zama wajibi a kansa, shi da Layla a matsayinsu na shugabannin ɗalibai na Kwalejin Zumunta, su tabbatar da sun kawar da wannan matsananciyar gaba da ke tsakanin iyayensu. Da jin haka sai Tafida da Ɗanjuma suka kalli juna. Su fa ba makafi ba ne. Sun san cewa haƙilon da Dauda yake yi har da nasa na kansa.

**Fitowa ta 3: A karƙashin gadar Sodangi**
Dauda, Layla

**DAUDA:** Layla, yaushe za ki koma makaranta?

**LAYLA:** Ka san fa Hassan ba wani sauƙi yake samu ba. Dole in zauna a wajensa. An riga an canza tunaninsa. Na karanta wata wasiƙa ma da ya rubuta, wai yana son ya mutu ya haɗu da mahaifiyarmu a aljanna. Kai Dauda! Wannan abin takaici har ina!

**DAUDA:** Ba kome! Ba kome Layla, yi haƙuri! Daina kuka! Na tabbata waɗannan manyan yaran sun yi amfani da shi ne kawai. Ya kamata mu san su waye. Na san kawai ingiza-mai-kantu suka yi masa.

**LAYLA:** Ai kuwa yana da alhaki a ciki. Dukkanmu ma, har da ni.

**DAUDA:** Na san da haka. Amma don Allah kar ki ɗau abin da zafi! Bari zan yi tunanin abin da ya dace. Ki je dai ki ci gaba da kula da Hassan, ma yi magana idan mun sami lokaci.

**LAYLA:** Ta yaya za mu haɗu tun da ga shi an hana mu ganin juna?

**DAUDA:** Mu dinga haɗuwa a ƙarƙashin gadar, ya fi sirri. Nunawa za ki dinga yi kamar kin fito motsa jiki ne. Za mu dinga haɗuwa a duk lokacin da ba kwa tare da Hassan. Kuma ki dinga komawa gida tun da hasken rana, kina yi kina sassarfa. Kin ga, haba, daina zubar da hawayen haka mana. Ko da kawuna ba shi da ra'ayin yafewa, na san babana zai yafe kome, saboda shi mai sarautar gargajiya ne, kuma da ma aikinsa ne ya taimaka wa jama'a. Haba Layla, zo mana! Share hawayen da suka cika kyawawan idanuwan nan naki mana! Haba Layla! Daina kuka mana!

**Fitowa ta 4: A ƙauye**

Dauda, Maigida Ranau

**DAUDA:** Ka ji dai yadda abubuwan suke, shi ya sa na zo wajenka neman shawara. Ta yaya kake ganin za mu iya taimaka wa Hassan? Su yanzu 'yan sanda suna can suna jiran su tsare shi da zarar ya samu sauƙi. Ni tambayar da nake wa kaina ma ita ce: To yanzu idan an raba yaro ɗan shekara goma sha biyu da gidansu, an je an ladabtar da shi, amfanin me wannan ladabtarwar za ta yi masa? Ni ina ganin sai dai ta ƙara tunzura shi ma.

**MAIGIDA RANAU:** To, ni yanzu wane irin taimako kake ganin zan iya yi?

**DAUDA:** Ni, Baba, so nake ka wayar min da kaina: wai tun da can kafin a ƙirƙiro irin waɗannan dokoki da kotunan da muke da su, wace hanya mai sarautar gargajiya yake bi ya yi hukunci?

**MAIGIDA RANAU:** E to, a irin wannan hali sai dai a sa a nemo shi yaron da dukkan mutanen gidansu, su zauna a gefe ɗaya, sannan sai a nemo waɗanda aka saɓa wa ɗin, wato su masu cocin da kuma kawunka Fada, su ma su zauna a ɗaya gefen. Ni kuma sai na zauna a matsayin alƙali, tare da dukkan jama'ata. Daga nan sai mu ji ta bakin ɓangarorin.

**DAUDA:** To, kana ganin za ka iya hukunta Hassan?

**MAIGIDA RANAU:** To, su dai waɗanda aka saɓa wa su ne za su zaɓi irin hukuncin da suke ganin ya da ce a yi. Mu kuma dattawan gari, mu ne za mu duba wannan hukunci mu ga ko ya yi tsanani ko kuma ya yi sassauci. Akwai ƙa'idoji na al'ada da ake bi wajen yin hakan. Kuma har yanzu muna yin irin wannan zama, amma don yin sulhu kawai a tsakanin waɗanda suka sami saɓani.

**DAUDA:** Kana ganin idan Kawu ya janye duk tuhumar da yake yi kome zai daidaita? Hasali ma dai, ai cocin ba duka ta ƙone ba.

**MAIGIDA RANAU:** Gaskiya ni da don ta ni ne ma, sai in ce ai ƙonewar da hannayen Hassan ma kawai suka yi, ya zamar masa hukunci.

**DAUDA:** Kana ganin Kawu zai amince da ra'ayinka?

**MAIGIDA RANAU:** E to. Ka san ai maganar coci ta shigo ciki, wanda kuma ka san gini ne mai daraja. Daɗin daɗawa, akwai kuma maganar

filin da duk ɓangarorin biyu suke taƙaddama a kansa. Abin fa ba mai sauƙi ba ne. Dole sai Hukumar Raya Kasa ta nemo wanda ke da haƙƙin mallakar wannan fili.

**DAUDA:** To, su kuma gidajen namu fa? Yaushe za su daina gaba da juna?

**MAIGIDA RANAU:** Ai ba wai gidajenku kawai abin ya shafa ba, har ma da al'ummomin nan guda biyu da ke wannan yanki gaba ɗaya. Ya zama dole kai da Layla ku jawo hankalin mabiya addinan nan guda biyu su zo a zauna don a tattauna da juna. Yanzu haka ma na samo wata ayar Alƙur'ani da na ji wani abokina Musulmi yana karantawa cewa: "Duk wanda za a hukunta, ya kamata a tabbatar ya aikata laifin". Yauwa, ga ta nan ma: "Idan mutum kuma ya yafe, ya nemi sulhu, to sakamakonsa yana wajen Allah." Shi ma kuma littafin Kirista na *bible* ga abin da yake cewa: "An albarkaci masu son yin sulhu. Kuma sakamakonsu shi ne gidan aljanna."

**MAI BA DA LABARI:**

To, a can ɗaya ɓangaren kuma Madam Titi, wato shugabar Kawalejin Zumunta, ta shawarci Dauda da ya zaɓo wata yarinyar da za ta tsaya a madadin Layla, tun da ana ganin za ta yi fashin sati biyu. Sai suka haɗu da wannan yarinya mai suna Maryam Tanko.

**Fitowa ta 5: A filin wasa na makaranta**

Maryam, Dauda, Tafida

**MARYAM:** Dauda, na yi farin ciki da muka haɗu da kai.

**DAUDA:** Haka ne, Maryam. Bai kamata mu bar Kungiyarmu ta Muhawara ta mutu ba haka kawai. Dole mu ci gaba da

muhawara a kan batu na gaba a cikin jerin batutuwanmu: Me ya sa ɗalibai, musamman dai mata yanzu, ba sa son ɗaukan darussan lissafi da kuma na kimiyya?

**MARYAM:** Gaskiya wannan tambayar tana da muhimmanci. Ni ma ina fa daga cikinsu. Don haka na cancani na fara muhawara a kan wannan batun.

**DAUDA:** Kina daga cikinsu? Ke kuwa me ya sa kike ganin haka?

**MARYAM:** To, a taƙaice dai, ni ina ganin ilimin kimiyya yana cin karo da faɗar Ubangiji.

**DAUDA:** To! Me ya sa kike ganin haka?

**MARYAM:** Ni na yi imani da cewa Ubangiji ya hallici sammai da ƙassai ne a cikin kwana bakwai. Kuma ni ina bin cocin da suke bauta wa Ubangiji ɗaya ne.

**DAUDA:** Lalle kam, kina da gaskiya. Ni kam na yarda da cewa an hallici ɗan Adam ne don ya yi bincike a kan kome. Kuma na gamsu da cewa wannan shi ne ainihin abin da ya kawo mu cikin duniyar nan, wato mu binciki abubuwa mu kuma yi tambaya don samun amsa. Kuma idan mun tattaro dukkan bayanai, sai mu yi aiki a kansu don mu gwada ingancinsu, idan kuma da gyara sai mu gyara.

**MARYAM:** In haka ne, ma ci gaba da wannan muhawara tare da sauran 'yan Kungiyarmu ta Muhawara!

**DAUDA:** To, sai an jima. *Phew! …* A! Yaya dai, Tafida?

**TAFIDA:** Gaskiya sai ka ɗan ƙara haƙuri fa, maigida Dauda. Yaya ka gani, ai tana da kyau ko?

**DAUDA:** Wa fa?

**TAFIDA:** Maryam mana, yarinyar da kuka gama magana da ita yanzu!

**DAUDA:** Au, ita kake nufi? Ai ni ban kula ba. Ni ban cika yanke hukunci da kamannin mutum ba.

**TAFIDA:** Haka ne. Zan tuna maka da wannan maganar da ka faɗa wata rana!

**DAUDA:** Mu yanzu abin da muka fi buƙata shi ne zaman lafiya ya dawwama a garin Sodangi! Ba ni mu tafa. Sai Sodangi kawai!

**DAUDA da TAFIDA**: Sodangi kawai!

**MAI GABATARWA:**
Wannan shi ne ƙarshen shirinmu na “Ji Ka Karu” a yau a kan “Haɗin kan mutanen Sodangi”. Nas Rakiya dai ba ta gajiya da kula da Hassan. Shi kuma Dauda ya fahimci yadda mutum kan zama shugaba mai adalci daga wajen mahaifinsa. Kuna iya sauraronmu a shiri na gaba don jin yadda za ta kaya. Kafin wannan lokaci kuna iya ziyartar adireshinmu na yanar gizo domin aiko da tsokaci ko kuma sake sauraron shirin, wato www.dw-world.de/lbe.